NAZARIN FASAHOHIN ZAMANI WAJEN KOYAR DA ADABIN HAUSA

Daga

Maryam Abubakar Ibrahim
Tsangayar Harsuna, Kwalejin Ilimi ta Birnin Tarayya Zuba, Abuja
Email: maryammashi2000@gmail.com

Fatima Lawal Sojo`
Tsangayar Harsuna, Kwalejin Ilimi ta Gwamnatin Tarayya, Katsina
Email: fadimatusoja@gmail.com
Da

Yusuf Ahmad
Tsangayar Harsuna, Kwalejin Ilimi ta Birnin Tarayya Zuba, Abuja
Email: dantanyajunior@gmail.com

Tsakure
Fasahohin zamani wasu sababbin hanyoyi ne da juyin zamani ya zo da su domin samun saukin fahimta ga masu koyo (dalibai), da kuma samun saukin koyarwa ga malamai. Samuwar wadannan hanyoyi da amfani da su ya kawo bunkasa da ci gaba kwarai wajen harkokin koyo da koyarwa a bangarorin ilimi da dama. Galibi irin wadannan fasahohi a kan same su ta hanyar yawan bincike da amfani da kirkirar na'urorin zamani, domin isar da sakon wani abu sabo daga mai koyarwa zuwa ga masu koyo a duk inda su ke ba tare da sun zo aji ko kuma wurin da aka tanada domin koyo da koyarwa ba, wato makaranta. Manufar wannan mukala ita ce fito da wadannan na'urori na fasahar zamani, tare da zakulo yadda ake amfani da su wajen koyo da koyarwa. An bi hanyoyi da dama wajen tattara bayanan wannan bincike wadanda suka hada da karance-karance da tambayoyi ga malamai masu koyarwa, da dalibai masu koyo a mabambantan fannoni na ilimi, sannan an shiga cikin yanar gizo-gizo domin binciko ire-iren wadannan na'urori na fasahar zamani da yadda ake amfani da su wajen koyo da koyarwa. Domin samun ingancin wannan bincike an dora shi a kan ra'in Jerantar Tunani na Jean Piaget (1896–1980) wanda ya samar a wajen shekarar 1964. Ra'in yana magana a kan a ba wa mai koyo dama yayi amfani da irin basira da ilimin da yake da su wadanda ya samu sakamakon mu'amalarsa da al'umma, wajen fahimtar wani sabon karatu (ilimi), fiye da yadda za a gaya masa wasu labarai ko bayanai. Ra'in ya samu karbuwa da magoya baya wadanda suka yi aikace-aikace da dama wajen assasa shi, kamar Lev Vygotsky da Jerome Bruner. Wannan ra'in yana da alaka ta kusa da wannan aiki, domin shi ne ya ba mu damar yin nazari ta hanyar amfani da sabbin dabaru ko fasahohi wajen ba wa dalibi dama ko taimaka masa ya fahimci karatu cikin sauki tare da samun dawwammammen karatu (ilimi). Adabin Hausa wani babban masaki ne wanda ya tattara muhimman abubuwan da suka shafi rayuwar Hausawa, wadanda suka hada da wakoki da kade-kade, tatsuniyoyi da labaran gargajiya, hikimomin Hausawa, kamar su azanci da sarrafa harshe, wasannin gargajiya da sauran abubuwan da Hausawa suka gada tun kaka da kakanni, har zuwa lokacin da suka samu ilimin karatu da rubutu. Daga karshe, wannan mukala ta gano irin yadda fasahohin zamani suke taka muhimmiyar rawa wajen saukaka harkokin koyo da koyarwa.

Muhimman kalmomi: *Fasahohi, Zamani, Koyo, Koyarwa, Adabin Hausa.*

1.0. Gabatarwa

A cigaba da sauye-sauyen da duniya ke fuskanta a fannonin ilimi da fasaha, ya zama wajibi a du ba yadda waɗannan sauye-sauye suka shafi koyar da adabin Hausa. Fasahohin zamani sun sauy a yadda ake kallon ilimi da koyarwa, inda aka samu sababbin hanyoyi masu sauƙaƙe fahimta da wadatar da ilimi ga ɗalibai da malamai. Adabin Hausa na daga cikin muhimman hanyoyi na ada na tarihi da al'adu, da kuma bayyana tunanin al'umma. Yayin da duniya ke ci gaba da bunkasa a fannin fasaha da sadarwa, koyar da adabin Hausa a matakin ilimi na buƙatar sauya salo da tsari domin ya dace da bukatu da dabi'un zamani. Wannan maƙala zata yi nazari kan yadda fasahohi n zamani (ICT – Information and Communication Technology) ke iya sauƙaƙa koyarwa da koy on adabin Hausa ta hanyar fahimtar yadda ake amfani da na'urori da manhajoji na zamani don sauƙaƙa isar da darasi, ƙarfafa fahimtar ɗalibai, da kare adabin al'ummar Hausa daga gushewa da kuma gabatar da wata manhaja ta zamani da za ta iya taimaka wajen wannan aiki.

1.1 Manufar Binciken

1 Maƙalar ta yi ƙoƙarin bayyana ma'anar fasahohin zamani da kuma alaƙarsu da tsarin koyar wa, musamman a fannin adabin Hausa.
2 Ƙoƙarin haskaka tasirin fasaha wajen sa koyo ya zama mai jan hankali, mai sauƙi da kuma mai dawwama.
3 Haka kuma taya nuni da muhimmancin amfani da fasaha wajen yaɗa nazarin adabin Hausa.

1.2 Ra'in Binciken

Wannan bincike ya yi amfani da Ra'in Jerantar Tunani na Jean Piaget (1896–1980), wanda ke cewa ɗalibai su koyi abubuwa ta hanyar amfani da tunaninsu da ƙwarewar da suka samu daga mu'amala da muhallinsu. Wannan ra'in yana da alaƙa da koyar da adabin Hausa, saboda yana buƙatar fahimta daga tushe, ba kawai bayar da bayani ba. Haka kuma, ra'in ya bada dama ga ɗalibi ya fahimci abin da ake koya ta amfani da hotuna da sautuka da hulɗa da kayan fasaha, maimakon ya tsaya jiran malamai su karanta masa a rubuce.

2.1 Adabin Hausa da Fasahar Zamani

Adabin Hausa na nufin tarin dukkan irin wallafe-wallafen da Hausa ke amfani da su wajen isar da sako da tunani da ilimi da al'ada da tarihi da falsafa ta hanyar baka ko rubuce. Wannan adabi na iya kasancewa a cikin salo na waƙoƙi da tatsuniyoyi da karin magana da almara da labarai da wasan kwaikwayo da sauran nau'o'in fasahar magana da rubutu da ke bayyana tunanin al'ummar Hausawa. Adabin Hausa yana da ginshiƙai biyu:

2.1.1 Adabin Baka

Wannan adabin shi ne nau'in adabi da ake yaɗawa ta hanyar magana kai tsaye daga bakin mutu m, ba tare da an rubuta shi a littafi ba. Wannan adabi ne da ke ɗamfare a cikin zuciya da harshe n a jama'a, ana yaɗa shi daga ƙarni zuwa ƙarni ta hanyar bak'in jama'a ta hanyar riwaya ko waƙa ko tatsuniya ko karin Magana ko kirari da sauransu. Siffofin Adabin Baka:

- Ba a rubuce yake ba: Ana yaxa shi ta baki daga mutum zuwa mutum.
- Mai sauƙin canzawa: Domin ba a rubuce yake ba, yana iya sauyawa daga wani mai labar i zuwa wani.
- Mai ɗauke da hikima da darussa: Galibin adabin baka yana koyar da tarbiyya, ladabi, tar ihi, ko darasi.

- Mai nishaɗantarwa: Ana amfani da shi don nishaɗantarwa da ilimantarwa, musamman a cikin yara.
- Na jama'a ne: Babu wanda zai ce shi ya ƙirƙira shi gaba ɗaya, domin yana rayuwa cikin al'umma.

Nau’o’in Adabin Baka:

- Tatsuniya: Labarai na ban dariya ko ban tsoro da ake bayarwa musamman ga yara da da ddare.
- Waƙa: Waƙoƙin baka kamar na biki, fada, aure, ko waƙar yabon jarumai.
- Karin Magana: Jimloli masu gajarta waɗanda ke ɗauke da ma’ana mai zurfi (misali: *jifar gafiyar Ɓaidu*).
- Kirari da Take: Kalaman yabon jarumai ko shahararrun mutane (misali: *Ɗan’aduwar d aji, mai zafin nama!*).
- Zantukan Hikima: Kalaman tunani da nasiha daga dattawa.

Muhimmancin Adabin Baka:

- Yana koyar da al’ada da tarbiyya.
- Yana ƙarfafa harshe da iya magana.
- Yana ajiye tarihin da ba a rubuce ba.
- Yana ƙarfafa tunani da fahimta musamman a yara.

Adabin Baka a cikin Adabin Hausa
A al’adun Hausawa, adabin baka shi ne ginshiƙi na farko da ke koyar da yara harshen Hausa, ɗa bi’un rayuwa da addini, da mutunci. Galibin waƙoƙin da ake raira wa jarumai, ko kuma labaran da ake bayarwa da daddare a gida, duk adabin baka ne.

Adabin Baka da Fasahar Zamani
Duk da cewa adabin baka a da ka ake aiwatar da shi a kuma adana shi da ka, amma hakan bai hana tasirin fasahar zamani a cikinsa ba. Daga cikin tasirin da fasahar zamani ta yi a adabin baka akwai:

- Naɗar waƙoƙin baka da tatsuniyoyi domin ajiye su.
- Watsa su ta YouTube da WhatsApp da Podcasts da sauransu.
- Nazarin su a jami’o’i domin kiyaye al’adu da harshen Hausa.

Adabin baka adabi ne mai ƙayatarwa da aka gada daga kakanni, wanda ke ɗauke da muhimman darussa, tarihi, da nishaɗi. Yana da matuƙar muhimmanci a fannin koyar da adabin Hausa, kum a yana buƙatar kulawa da amfani da fasahar zamani domin a kare shi daga ɓacewa.

2.1.2 Adabin Zamani Adabi
n zamani wani muhimmin reshe ne na adabi wanda ya fara bayyana a cikin rubuce-rubuce da ka yayyakin wallafa na zamani, musamman daga lokacin da Hausawa suka fara rubutu da amfani d a haruffan Boko da Ajami. Shi wannan adabi yana amfani da na’urorin zamani da harshe na za mani, yana kuma ɗauke da sabbin salo da ra’ayoyi da tsarin rayuwa da ke bayyana irin canje-ca njen da al’umma ke fuskanta a zamani.

Siffofin Adabin Zamani

1. A rubuce ne, ba baka ba: Ba kamar adabin baka ba, adabin zamani ana rubuta shi ne a litt attafai, mujallu, jaridu, da yanar gizo.
2. Na zamani ne a salo da ra'ayi: Yana ɗauke da ra'ayoyin zamani irin su demokuradiyya, 'yancin ɗan Adam, yaki da talauci da cin zarafi da sauransu.
3. Harshe mai sauƙi da nishaɗi: Ana amfani da harshe da kalmomi da suka dace da zamani, kuma da sauƙin fahimta.
4. Yana amfani da kafofi na zamani:Misali: littattafan e-book, fina-finan adabi, rediyo da ta labijin, da shafukan yanar gizo.
5. Yana sarrafa kowane jigo: Har da na soyayya da siyasa da ilimi da rayuwar yau da kullu m da zamantakewa da sauransu.

Nau'o'in Adabin Zamani

1. Littafin ƙagaggun labarai (novels)—Irins "Ruwan Bagaja" na Abubakar Imam ko "Magan a Jari Ce."
2. Gajerun labarai (short stories)—Waɗanda ke bayyana darasi ko nuni cikin taƙaitaccen lo kaci.
3. Waƙoƙin zamani—Irin su waƙoƙin da ke bayyana zamantakewar yau da siyasa ko addini cikin salo mai nishaɗi.
4. Finafinai (Kannywood)—Waɗanda ke cike da adabi, kamar "Sangaya," "Labarina," da "Izzar So." Da sauransu
5. Drama da wasan kwaikwayo – A fage kamar rediyo, TV ko a dandalin makaranta.

Muhimmancin Adabin Zamani

- Yana isar da sakonni cikin sauri da inganci.
- Yana taimakawa wajen watsa ilimi da jaddada dabi'u.
- Yana zama madubi ga al'umma wajen yin nazari a kan halaye da canjin zamantakewa.
- Yana zama kayan koyarwa a makarantu.
- Yana bunkasa fasahar rubutu da karatu.

2.2 Fasahar Zamani da Koyar da Adabi

Fasahohin zamani na nufin sababbin dabaru ko na'urorin da ke taimaka wajen sadarwa, adanawa, da yaxa ilimi ta hanyar amfani da kwamfuta ko intanet ko wayar zamani (smartphone), aikace-aikacen koyarwa, da sauran kayan fasaha da ke sauƙaƙa sadarwa da fahimtar darasi. Wadannan fasahohi sun haifar da ci gaba mai yawa a fagen ilimi ta yadda ba lallai sai ɗalibi yana cikin aji kafin ya amfana da karatu ba. A koyarwa, waɗannan fasahohin suna da fa'idodi kamar haka Sauƙaƙa koyar da batutuwan adabi cikin kallo da sauraro da ƙarfafa fahimta ta amfani da hoto da sautuka da motsi da samar da hanyoyin yin aikin gida ta kan lokaci da inganta koyo mai zaman kansa (self-directed learning). Fasahar zamani ta sauya yadda ake kallon ilimi da hanyoyin koyarwa gaba ɗaya. A fannin koyar da adabi, wannan sauyi ya fi bayyana ne wajen sauƙaƙe fahimta, isar da darussa cikin sauri da sauƙi, da kuma ƙarfafa shiga kai tsaye tsakanin malamai da ɗalibai. Kamar yadda ake buƙatar gani, ji, da fahimta a cikin koyar da adabi, haka fasahar zamani ke samar da kayan aiki da tsari da zai taimaka wajen sauƙaƙa waɗannan buƙatu. Daga cikin abubuwan da fasahar zamani wajen koyar da adabin Hausa ya shafa sun haɗa da:

2.2.1. Inganta Hanyoyin Koyarwa

Fasahar zamani ta ba da damar yin amfani da kayan gani da ji kamar bidiyo, sauti, da kwasfan fayiloli (podcasts), waɗanda ke sa ɗalibai su fi fahimtar darasi da sauri fiye da karatu kawai

daga littafi. Alal misali, sauraron waƙar baka ko kallon wasan kwaikwayo ta bidiyo zai sa ɗalibi ya fi fahimtar salon magana, al'ada, da ƙa'idodin adabin gargajiya.

2.2.2. Sauƙaƙa Fahimta da Maida da Hankali

Tare da amfani da kayan fasaha, malamai na iya amfani da zane-zane ko taswira da rubuce-rubuce na gani waɗanda ke taimaka wa ɗalibai su fahimci abubuwan da ake koya da kyau. Wannan yana da amfani musamman a cikin darussa na waƙoƙi, tatsuniyoyi, da labaran gargajiya inda amfani da jin sauti da kallon yanayi ke taimakawa wajen fahimtar salo da ma’ana.

2.2.3. Dama ga Koyo a kowane Lokaci

Fasahar zamani kamar intanet da manhajojin wayar salula sun ba ɗalibai damar koyo ko da ba su a cikin aji. Wannan ya ƙara yawan damar da ɗalibai ke da ita wajen samun darasi da yin maimaitawa yadda suka ga dama.

2.2.4. Ƙarfafa Bincike da Rubuce-Rubuce

A fannin binciken adabi, fasahar zamani ta samar da abubuwa kamar e-books, dijital ɗin waƙoƙi da labarai, da kuma zaɓaɓɓun bayanai da ke kan intanet. Wannan yana taimaka wa ɗalibai da malamai wajen gudanar da bincike da kuma rubuce-rubuce cikin sauƙi da sauri.

2.2.5. Haɓaka Hulɗa da Aiki Tare

Manhajojin koyarwa da sadarwa kamar Google Classroom, Zoom, da WhatsApp sun haɓaka hulɗar ilimi tsakanin malamai da ɗalibai. Haka kuma, ana iya gudanar da tattaunawa da bita cikin sauƙi, wanda hakan ke ƙara jan hankalin ɗalibi ga darasin adabi.

2.2.6. Kare Adabin Gargajiya Daga Gushewa

Ayyukan adabin baka na da rauni wajen gushewa idan ba a ɗauke su ba cikin kayan adana fasaha. Fasahar zamani tana ba da damar rikodin waƙoƙi, tatsuniyoyi, da azancin baka, wanda hakan ke taimaka wa wajen adana su don ƙarni masu zuwa.

2.2.7. Sauya Matsayin Dalibi Daga Mai Sauraro Zuwa Mai Halarta

Ta amfani da fasaha, ɗalibai ba su ƙara kasancewa masu sauraron darasi kawai ba, sai dai sun zama masu shiga kai tsaye wajen ƙirƙira da tattaunawa da raba ra’ayoyinsu. Wannan yana haifar da zurfin fahimta da haɓakar basira a cikin adabi.

2.3. Nau’o’in Fasahohin Zamani da Aikace-aikacensu

- Kwamfuta da Manhajojinta: Ana amfani da manhajojin kamar Microsoft PowerPoint, Audacity, da Canva wajen gabatar da waƙoƙi da zane-zane, ko azanci cikin salo mai jan hankali.
- Intanet da Yanar Gizo: Ana amfani da dandali irin su YouTube, Wikipedia, da Google Classroom wajen watsa darussa da koyarwa.
- Wayar Salula (Smartphone): Manhajojin koyarwa kamar Duolingo, Google Lens da Vo ice Recorder na taimakawa wajen fahimtar karin harshe da sarrafa adabi.
- Allon Gwaji na Zamani (Interactive Whiteboards): Ana amfani da su wajen nuna bidiyo ko karanta rubuce-rubuce da zayyana taswira ko zane a aji.

2.4 Dalilan da ke Tabbatar da Bukatar Fasahar Zamani Wajen Koyar da Adabin Hausa

- Saukaka Samun Abubuwan Karatu: Fasahar zamani na ba da damar adana wakoki da tatsuniyoyi cikin bidiyo, sauti, ko rubuce a intanet da sauran na'urori.
- Haskaka Sautin Baka da Alamomin Zamani: Wakar baka tana da sauti, murya, da motsi. Amfani da fasaha kamar bidiyo ko rediyo yana ba da cikakken tsinkaye da fahimta.
- Tallafa wa Malamai da Dalibai: Ana iya amfani da kayan fasaha wajen gabatar da darasi mai ma'ana da jan hankali, musamman ga yara da matasa.
- Kare Adabin Hausa daga Gushewa: A zamanin da mutane ke yawan dogaro da yanar gizo, fasaha na taimakawa wajen adana adabi cikin tsarin dijital.
- Samar da Damar Bincike da Ingantaccen Nazari: Aikace-aikace kamar Wikipedia, JSTOR, ko Hausa Online Resources suna ba da damar binciken adabin Hausa daga ko ina.
- Bude Tattaunawa da Huldɗa tsakanin Ɗalibai da Malamai: Ana iya amfani da Zoom, Google Classroom, da WhatsApp domin karfafa musayar ra'ayi kan rubuce-rubuce da wakoki.
- Inganta Ƙwarewar Rubuce-rubuce da Karatu:Aikace-aikacen kamar Grammarly, Google Docs, da Text-to-Speech suna saukaka fahimta da aikin karatu.

2.5. Tasirin Fasahohin Zamani a Kan Koyo da Koyarwa Wadanna n fasahohi sun kawo gagarumin sauyi a harkar koyo da koyarwa:

- Sun rage takura ga ɗalibai wajen samun littattafai da malamai.
- Sun kara ma malamai dama wajen amfani da sabbin dabaru.
- Sun bada dama ga ɗalibai su koyi adabin Hausa ta nishaɗi da sauki.
- Sun sa koyo ya wuce aji ya koma gidaje da sauran wurare.

2.6. Gudummawar Fasahohin Zamani ga Adabin Hausa Ada bin Hausa na da yalwar nau'o'i kamar wakoki, tatsuniyoyi, hikimomi, da labaran gargajiya. Am fani da fasahohin zamani:

- Ya ba da damar ajiye da watsa wakokin baka.
- Ya taimaka wajen gyara rubuce-rubuce na adabin Hausa.
- Ya taimaka wajen gudanar da bincike a kan wakoki da tatsuniyoyi.
- Ya bai wa ɗalibai damar sake sauraro da karanta darussa a duk lokacin da suke so.

2.7. Kalubale da Matsaloli
Akwai ƙalubale da matsaloli da amfani da hanyoyinn zamani wajen koyar da harshen Hausa ke fuskanta daga cikin su akwai:

- Rashin isassun kayan aiki a makarantu da jami'o'i.
- Karancin ilimi ko ƙwarewa a fannin amfani da fasaha daga bangaren malamai da ɗalibai
- Matsalolin sadarwa da wutar lantarki a wasu yankuna.

2.8 Sakamakon Bincike
A ƙarshe wannan binciken ya gani cewa, fasahohin zamani suna da matukar tasiri wajen saukaka koyarwa da fahimtar adabin Hausa, musamman ta hanyar amfani da hotuna da sautuka da bidiyo, da aikace-aikacen zamani. Kuma an gano cewa amfani da fasaha a aji yana ƙara jan hankali da sa ɗalibai su fi son karatun adabi, musamman idan aka haɗa shi da sautuka da gani kamar wakoki da tatsuniyoyi da finafinai na gargajiya. Sannan malamai suna samun dama su sauya salon koyarwarsu daga karanta littafi kawai zuwa amfani da kwamfuta da internet da sauran manhajoji, wanda hakan ke inganta ilimi da kuma sa malamai su zama masu zamani.

Sannan binciken ya gano fasahar zamani ta taimaka wajen wadatar da kayan koyo kamar bidiyo, fayilolin sautuka, da littattafai na lantarki (e-books) da ke cikin manhajoji da shafukan intanet. Tare da tabbatar da cewa ɗalibai na iya koyan darussa ba tare da zama a cikin aji ba, ta hanyar amfani da fasahar zamani musamman a lokutan hutu ko rashin malamai.
Wani abu da binciken ya ƙara ganowa shi ne, fasahar zamani na bai wa ɗalibai masu buƙata ta musamman damar samun ilimi cikin sauƙi, misali, ta amfani da murya maimakon rubutu ko bidiyo maimakon karatu. Sannan an gano cewa fasahar zamani tana taimaka wa ɗalibai da malamai wajen gudanar da bincike cikin sauƙi da kuma rubuta takardu na ilimi da adabi cikin salo mai kyau da na zamani.
Daga ƙarshe binciken ya gano yadda fasahohin zamani ke iya koyar da adabi ta hanyar podcast da YouTube da WhatsApp group, e-learning platforms, da sauran hanyoyin zamani masu amfani.

2.9 Shawarwari

Wannan bincike yana bada shawara domin inganata amfani da fasahar zamani wajen koyar da harshen Hausa kamar haka;

- A samar da kayan aikin zamani a makarantu.
- A horar da malamai da ɗalibai kan yadda ake amfani da fasahohi.
- A karfafa haɗin gwiwa da cibiyoyin fasaha da ilimi.
- A ƙarfafa bincike da rubuce-rubuce na adabin Hausa ta amfani da fasahar zamani.

2.10 Kammalawa

Binciken nan ya tabbatar da cewa amfani da fasahohin zamani wajen koyar da adabin Hausa ba wai zaɓin ci gaba ba ne kawai, illa wajibi ne a yau. Adabin Hausa yana da yalwar nau'o'i da salo waɗanda ke buƙatar fahimta ta hanyar gani, ji, da karatu. Hakan yasa amfani da na'urori kamar kwamfuta da intanet da rediyo, da bidiyo ke taimaka matuƙa wajen sauƙaƙa koyarwa da fahimta r adabin Hausa. Binciken ya kuma nuna cewa fasahohin zamani sun buɗe ƙofofi na samun ilimi a sauƙaƙe, sun kuma ƙarfafa hulɗar kai-tsaye tsakanin malamai da ɗalibai. Duk da cewa akwai ƙalubale irin su rashin kayan aiki, ƙarancin horo, da matsalar sadarwa, amma akwai fata da dama idan aka ɗauki matakan da suka dace. Don haka, wajibi ne a bunƙasa amfani da fasahohin zamani a kowane matakin ilimi domin ƙarfafa harshen Hausa da adabinsa, ta yadda za a tafiyar da al'adu da ilimi cikin zamani.

Manazarta

Afolabi, A. (2019). *ICT and Language Learning: Potentials and Pitfalls*. Adeko Publishers.

Mustapha, A. S. (2022). The Role of Digital Technology in Promoting Indigenous Literature. *A frican Journal of Language and Literature, Vol. 11*.

Piaget, J. (1952). *The Origins of Intelligence in Children*. International Universities Press.

Sa'id, B. A. (2020). Sabbin Hanyoyin Koyar da Harshe da Adabi a Makarantun Sakandare. Kad una: Alkalam Books.

Usman, M. I. (2017). Amfanin Wayoyin Salula Wajen Koyar da Harshe da Adabi. *Nigerian Jo urnal of Educational Technology, Vol. 9,* No. 1.

Yusuf, M. A. (2018). Fasahar Sadarwa da Tasirinta ga Koyo da Koyarwa a Najeriya. Mujallar Nazarin Harshe da Ilimi, Vol. 5, No. 2.

Yahaya, I.Y. da wasu (2006). *Darussan Hausa don manyan makarantun sakandare* University Press PLC